# Ku cika sawun gaba, sannan wanda ke biye da shi, abin da aka samu tawaya daga gare shi to ya zama a cikin sawun ƙarshe ne

Daga Anas Ibnu Malik - Allah Ya yarda da shi - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: «Ku cika sawun gaba, sannan wanda ke biye da shi, abin da aka samu tawaya daga gare shi to ya zama a cikin sawun ƙarshe ne».
[Ingantacce ne] [Abu Dawud da Nasa'i ne suka ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya umarci mazaje masu yin sallah a jam'i da cika sawun farko, sannan da cika sawun da ke biye da shi, idan za’a samu wata tawaya a cikin wani sawu to wannan tawayar ta zama a sawun ƙarshe ne.

https://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/65738